**SHIRIN ALLAH NA DOGON LOKACI - Babi na 1 - 5**

Wasu annabawa sun kai saƙon Allah ga mutanensa, amma Habakuk yana magana ne da Allah a lokacin da yake ƙoƙarin fahimtar dalilan da ya sa mugunta yake karuwa sai ka ce Allah bai ɗauki matakin yin wani abu ba.

Allah ya nuna wa annabinsa abu biyu da za su faru: za a hukunta kowane mai aikata zunubi kuma halin Allah ba ya sakewa. Yana iya yin shiru na wani lokaci, amma zai aikata nufinsa. Habakuk ya "ga" ɗaukakar Allah sai halinsa ya sake. Allah yana bukatar mutanensa su yi rayuwa ta bangaskiya don gaba na Allah ne.

# Babi na 1 Shirin Allah: Domin Nan Gaba

## Farawa 50:15-21

GABATARWA MINTI 5

**MANUFA:** Domin a tabbatar mana a kuma ƙarfafa mu cewa Allah yana da shiri mai kyau domin waɗanda suka dogara gare shi.

Yanzu da muke shigan wata shekara, wannan ya ba mu zarafi mu duba abin da Allah ya yi a rayuwarmu mu kuma duba abin da ya koya mana game da kansa a watannin da suka gabata.

Waɗanne abubuwa ka koya game da Allah da ya ba ka ƙarfin hali na dogara gare shi nan gaba?

A wannan nazari za mu dubi ayoyi a ƙarshen surar Farawa inda aka yi magana a kan Yusufu. Yusufu yana da damuwa sosai, amma ya yi nasara a rayuwa, domin ya san Allah Rayayye. Wannan ya ƙarfafa shi ya san cewa Allah yana da iko bisa dukan abubuwan da ke faruwa kuma wannan ya ba shi bege mai kyau game da nan gaba.

TAMBAYOYIN TATTAUNAWA MINTI 30

**Karanta Farawa 50:15-17**

**Rashin Dogara yakan sa tsoro:**

1. Wane mataki Yusufu ya ɗauka game da 'yan'uwansa tun da suka isa Masar? Karanta Farawa 47:11-12, 27.

2. Waɗanne abubuwa biyu ne 'yan'uwan nan suke tsoro bayen mutuwan mahaifinsu Yakubu (aya 15)? Menene ainihin dalilin da ya sa suke tsoro?

3. A tunanin ka don me Yusufu ya yi kuka lokacin da ya ji sako daga 'yan'uwansa (aya 17)?

**Karanta Farawa 50:18-21**

**Tanadin Allah domin nan gaba:**

4. Don me yan'uwan suka faɗi ƙasa a gaban Yusufu kuma suka saɗaukar da kansu a gabansa (aya 18)?

## CI GABA DA TAMBAYOYI

Me ya sa a tunaninka tubarsu ta zama ta gaske a wannan lokaci?

5. Ta yaya Yusufu ya nuna fahimtar ayyukan Allah da ikonsa bisa rayuwarsa ta wurin yadda ya yi magana da yan'uwansa (aya 19-20)?

6. Waɗanne abubuwa uku ne Yusufu ya yi wa 'yan'uwansa (aya 21)?
   Ta yaya wadannan ayyukan alheri suka bayyana manufar Yusufu da dogaransa ga Allah don nan gaba?

7. Idan za ka dogara ga Allah domin sakamako, wane bambanci wannan zai yi a halinka da abin da za ka yi lokacin wahala ko dangantakarka?

## TAKAICIN KOYARWA MINTI 5

Yan'uwan Yusufu sun koma Masar bayan sun binne mahaifinsu (Far. 50:7-9). Ba baƙin ciki suke cike da shi kaɗai ba, amma suna tsoro. Babban damuwarsu ita ce na zunubin da suka yi shekaru da yawa da suka gabata. Yanzu da Yakubu ya mutu ba su da wanda zai kare su a baƙuwar ƙasa idan Yusufu ya ce zai rama abin da suka yi masa. Wannan ne dalilin da ya sa suka shirya ƙarya wanda a ganinsu zai kare su.

Ko kukan da Yusufu ya yi, ya yi shi ne da ɓacin zuciya yayin da ya ga suna ƙoƙarin yin ƙarya da rashin nuna masa yarda? Me ya yi don ya ƙara musu wannan tsoro a zukatansu? Cikin abubuwan da Yusufu ya yi, ya nuna halaye irin na Almasihu:

1. Ya bar wa Allah hukuncin mugunta (aya 19).
2. Ya ga Allah yana aiki cikin abubuwan da ke faruwa, har ma a cikin muguntar da su 'yan'uwansa suka yi (aya 20).
3. Ya aikata alheri da ƙauna ga yan'uwansa ko da yake sun yi masa mugunta (21)

Yusufu ya sha wahala a rayuwarsa amma da ya fahimci kasancewar Allah da ayyukansa, wannan ya kawar masa da baƙin ciki. Maimakon da muguntar da iyalinsa suka yi masa ya ƙara ɓata masa rai, ya ga abin da 'yan'uwansa suka yi masa ta wani fanni, sai ya yi ƙoƙari ya ƙarfafa su don su yarda da shi, su kuma dogara ga Allah mai biya musu bukata nan gaba.

## AIKATAWA MINTI 20

A rabu cikin ƙungiya biyu ko fi. A tattauna tambaya ɗaya sa'an nan a yi addu'a.

1. Wani ɗan Ikilisiya ya rasa aiki inda yake samun kuɗi mai yawa. Bayyana yadda za ka ƙarfafa shi don ya dogara ga Allah a nan gaba.
2. Akwai damuwa a iyali saboda zancen fili. Ta yaya dogararka ga Allah a kan shi mai tanadawa ne domin nan gaba zai shafi halinka ga danginka?

**WAKA:** "Dogara ga sunan Yesu...."

**ADDU'A:**

* A gode wa Allah saboda akwai tabbacin aikinsa na alheri a rayuwarmu.
* Yi addu'a domin samun taimako don mu nuna cewa mun dogara gare shi domin nan gaba da samun ikon taimakon wasu da suke cikin wahala.

**HADDACEWA:** Farawa 50:20-21a.